# Littafi mai Tsarki na yara

## Ke gabatar da

# Yesu ya Warkar da Makaho



Wanda ya Rubuta: Edward Hughes

Mai Zane: Janie Forest
Alastair Paterson

Mai niyyan daukan nauyi: Ruth Klassen

Fassarawa: Bible Society Nigeria

Wanda ya Wallafa: Bible for Children
www.M1914.org

©2023 Bible for Children, Inc.

Zaku iya kofan wanna labarin ku wallafa idan
har ba zaku sayar da shi.

Batimayus makaho ne, yana zama a bakin hanya kusa da Yeriko. Yana roko. ‘Yan tausayi wadanda suka ba shi sadaka ko dan abinci yayinda suke wucewa. Batimayus bai iya aiki ba saboda ba ya gani. Yana roko ne kawai.



**Wata rana, hanyar ya kasance da mutane da yawa. Batimayus ya ji takawar kafafun mutane da yawa. Wani abu wanda ba a saba da shi ba yana faruwa. Ba a dadde ba sai makahon ya gane abin da ke faruwa.**



**Yesu daga Nazaret yana a gari. Taron jama'a sun taru domin su ga Yesu, su saurare Shi.**





"Yesu, Dan Dawuda, yi mini jinkai!" Don me Batimayus ya yi kuka da karfi? Don me ya yi tunani cewa Yesu zai taimake shi? Watakila ya riga ya ji labari game da yadda Yesu ya warkar da wadansu. Wadansu kurame ne, wadansu bebaye ne, wadansu guragu ne – wadansu kuma makafai ne, kamar yadda shi ma yake. "Dan Dawuda, yi mini jinkai," Batimayus yana ihu a kai a kai. Muryarsa tana kara da bege.



**Batimayus yana da tabbacin abu guda daya. In bai sami taimako yanzu ba, watakila ba zai sake sami iri wannan zarafi ba. Watakila Yesu ba zai sake bin wannan hanya ba.**



Dole sai Batimayus
ya kai wurin Yesu.
Amma mutanen sun
ki su matsa masa.
“Shsssssssssh!”
suka ce masa.  Sun
ja masa kunne
domin ya yi shiru.



**Amma Batimayus ya ki ya yi shiru. Ya ci gaba da ihu. Nan da nan sai Yesu ya tsaya! Ya saurara! Ya umarta a kawo mishi makahon a wurin shi.**



Ya jefar da rigarsa a gefe, Batimayus
ya tashi ya zo wurin Yesu.



**“Mene ne kake so in yi maka?” Yesu ya tamabaya. In kai ne yaya za ka amsa? Ko da ka tambaye shi kudi sosai, ko riguna masu kyau sababbi? Abin da Batimayus ya tambaya kenan ne?**



A’a, Batimayus makahon bai tambayi Yesu
Zinariya ko riguna masu kyau ba.
Ka san abin da yake so.



“Ubangiji, ina so in sami ganina.” Batimayus ya so idanunsa su bude. Ya ga itatuwa da tsuntsaye da duka kyawawan halittun Allah. Ya so ya sami gani domin ya lura da kansa domin kada ya zama maroki.



Sai Yesu ya ce wa Batimayus: “Karbi ganinka. Bangaskiyarka ta cece ka.”



Nan take ya sami ganinsa, ya bi Yesu. Iyakacin abin da zai iya fada shi ne “Allah abin mamaki ne! Ya warkar da ni!”  Lokaci ne na abin mamaki ga Batimayus.





**Duka mutanen, sa’ad da suka ga abin da ya faru, suka yabe Allah. Sun sake ganin abin mamaki na ikon Dan Allah, Yesu, ta wurin kawo gani ga wani taliki makaho maroki.**

# Yesu ya Warkar da Makaho

Tahiri da ga maganar Allah, littafi mai Tsarki

a na samu a

Markus 10, Luka 18,
Yohanna 9

"Shigowar maganar ka yana baduar kawo haske." Zabura 119:130

# KARSHE

Wanan tahiri daga littafi mai-tsarki na mana bayanin Allah mu wanda ya halicce mu wanda yake son mu san shi.

Allah ya san da cewa mun yi abubuwan da ba su da kyau, wanda yake kira zunubi. Sakamakon zunubi mutuwa ne, amma Allah ya na kaunan mu sosai. Ya aiko da Ɗansa Yesu, ya mutu a kan giciye ya sha wahala domin zunuban mu. Kuma sai Yesu ya tashi daga matattu ya koma gida a sama. Idan ka bada gaskiya ga Yesu. Ka roƙeshi gafaran zunuban ka, zai yafe. Kuma zai zo ya zauna a cikin zuciyan ka kaima kuma zaka zauna a zuciyar shi har abada.

Idan ka yadda da wannan gaskiya ne, Ka cewa Allah:
Ya Yesu, na bada gaskiya kai Allah ne, ka kuma zamu mutum don ka mutu domin zunubi na, kuma yanzu ka tashi. Ina roƙon ka, ka shiga cikin zuciya na kuma ka yafe min zunubai na, Domin in samu sabon rai yanzu, kuma wata rana in zauna tare da kai har abada. Ka taimake ni in yi maka biyayya kuma in yi rayuwan da zai gamshe ka a matsayin ɗan ka. Amin.

Ka karanta littafi mai-tsarki kuma ka yi magana da Allah a kulla yaumin. Yahaya 3:16